*Appendix30:*

# JIHADI A MUSULUNCI

**Sheikh Aminuddeen Abubakar**[1]

## Gabatarwa

Dukkan yabo ya tabbata ga Allah, Sarkin da Ya yi umarni da yin Jihadi domin tsarakake kasa ga barin kafirci da kafirai, kuma ga barin barna da masu barna. Allah (T.W.T.) Ya yi alkawari ga masu Jihadi cewa za su sami babbar lada, da babban sakamako.

Ina shaidawa babu wanda za a bauta masa da cancanta sai Allah, Shi kadai dinsa, ba Shi da abokin tarayya. Ina shaidawa Annabi Muhammad (S.A.W.) Bawan Allah ne, Ma'aikin Allah ne; shi ne Annabin da ya yi Jihadi domin daukaka kalmar Allah hakikanin Jihadi. Ya yi Jihadi da zuciyarsa, ya yi da bakinsa, ya yi kuma ta hanyar kira da bayani. Sannan ya yi Jihada da takobi, ya kuma yi da kaifin kansakali. Saboda haka, rayuwarsa (S.A.W.) dukkaninta Jihadi ne. Sannan dukkanin lokatansa, cikin kyautata rayuwar alumma ya ke, da kuma shiryar da hanya madaidaiciya; Allah (S.W.T.) Ya kara tsira da aminci a gare shi, da 'ya'yan dakinsa, da Sahabbansa wadanda suka sayar da ransu, da dukiyarsu domin su yi Jihadi a daukaka kalmar Allah; suna masu biyayya a gare shi, kuma suna masu neman ladarsa. Allah (S.W.T.) Ya kara tsira da aminci a garesu da garemu ga baki daya.

## Yin Jihadi Wajibi Ne A Kowane Musulmi

Bayan haka, ya bayin Allah! Ku ji tsoron Allah ku yi biyayya ga Allah, ku sani Allah Ya umarce ku da yin Jihadi domin daukaka tafarkinsa. Wannan umarni da Allah Ya yi, umarni ne wajibi, kuma na tilas abin karfafawa. Wajabcin Jihadi yana dada karfafa a kowane zamani, a kuma kowane guri; za a yi jihadin ne da rai, da dukiya a duk lokacin da:

i. Kafirai suka yi niyyar tsawwala wa Musulmi,
ii. Kafirai suka halatta zubar da mutuncin Musulmi,
iii. Kafirai suka keta alfarmar Musulmi,
iv. Kafirai suka wulakanta Musulmi,
v. Kafirai suka take daraja, da karamar Musulmi da kafafuwansu,
vi. Kafirai suka yi fito-na-fito da Musulmi wajen bayyana adawa, da gaba,
vii. Kafirai suka rinka kulla makirci da sharri ga Musulmi.

Irin wadannan abubuwa, su ne suke gudana tsakanin Yahudawa da Musulmin Falasdinu, kuma irinsa ne yake gudana a tsakanin 'yan Kwaminis da 'Yan Afghanistan; hakanan za ka tarar da kasashe masu dimbin yawa ta yadda 'Yan Mishan suke kulla irin wannan makirci ga Musulmin wannan gurin.

---

[1]A. Abukakar, 9-23 Dec/88.

**Lokacin Da Jihadi Ya Wajaba**

Ya wajaba a yi yakin ne da dukiya, da kuma rai a duk lokacin da kafirai suka fara kashe Musulmi; ya zamana suka kulle muguwar niyyah da makirci game da Musulmi, kuma suka zama sun fara dukan mutanen kasa wadanda suke amintattu, ba su zagi kowa ba, ba su cuci kowa ba, ba su mari kowa ba. To, idan kafirai suka aikata daya daga cikin irin wannan dalilai da suka gabata, to, wajibi ne akan kowane Musulmi na duk duniya ya yi yaki, kuma zai yi yakin ne a bayan shugaba na Addinin Musulunci.

Sannan yakin yana dada wajaba akan kowa da kowa idan Limamin Musulmi ya ce a fita ga baki daya. Saboda haka, Jihadi a Addinin Musulunci, hakki ne na Addinin Musulunci. Idan dai mutum Musulmi ne, to, wajibi ne ya sauke wannan hakki da yake kansa.

## HANYOYIN YIN JIHADI

i. **Yin Jihadi Da Rai –** Ana yin Jihadi da rai, wato mutum ya fita da kansa, ya ba da ransa. Sannan ana yin yakin da kudi, wato mutum ya bayar da dukiyarsa domin daukaka kalmar Allah.

ii. **Yin Jihadi Da Harshe –** Sannan kuma ana yin yakin da harshe; shi ne mutum ya yi magana da bakinsa, kamar mutum ya fada da bakinsa ta yadda zai kwadaitar da mutane sha'anin yaki da Jihadi.

iii. **Yin Jihadi Ta Hanyar Tattaunawa –** Sannan ana yin Jihadi ta hanyar tattaunawa a game da yadda za a yi Jihadin. Duk wanda ya shiga aka tattauna da shi, to, shi ma kamar ya yi Jihadin ne.

iv. **Yin Jihadi Ta Hanyar Leken Asiri –** Sannan ana yin Jihadi ta hanyar shirya 'yan leken asiri, wadanda za su rinka shiga cikin arna domin su binciko sirrinsu, da abubuwan da suka boye; duk wanda ya shiga cikin wannan kungiya ta leko asirin kafirai, to, shi ma ya yi Jihadi.

v. **Yin Jihadi Ta Hanyar Karfafa Guiwar Muminai –** Sannan ana yin Jihadi ta hanyar yadda za a karfafa guiwar Muminai akan yin yaki; ta hanyar yin huduba, da yin bayani a rediyo da talabijin, da rubutu a jaridu da mujalloli.

vi. **Yin Jihadi Ta Hanyar Tara Dukiya Ga Masu Jihadi –** Sannan ana yin Jihadi ta hanyar zaburar da Musulmi ta yadda za su tara dukiya domin a kai taimako ga masu Jihadi, kuma a kai kayan abinci ga iyalan masu Jihadi. Duk wadannan hanyoyi da suka gabata, kowannensu hanya ce ta Jihadi, duk wacce mutum ya yi, ya zama mujahidi fiye sabiylillah.

## ZAMA CIKIN SHIRI A KO DA YAUSHE

Shirya kayan karfi, da kayan fada, da kayan tanadi a kowane lokaci, wajibi ne idan dai Musulunci yana aiki a cikin zukatan Musulmi. Allah (T.W.T.) Ya fada a cikin Surah al-Anfal, aya ta sittin (60) cewa: "Ku yi musu tanadin abin da kuka sami iko na daga karfi, da tsaron dawakai (kayan yaki) wanda za ku saka barazana a cikin zukatan abokan gaban Allah, kuma abokan gabarku. Da wadansu (arnan) wadanda suke bayan wadancan, wadanda ku ba ku san su ba, amma Allah Ya sansu. Duk wani abin da kuka

ciyar, domin (Jihadin) daukaka kalmar Allah, Allah zai cika muku ladarku; ai ku ba ta yadda za a yi a zalunceku." (Al-Anfal 8/60)

Saboda haka, ya jama'a, za mu ga a wannan Ayah, Allah (S.W.T.) Yana cewa "Ku yi musu tanadi." Wannan ai, umarni ne. To, idan Allah (S.W.T.) Ya yi umarni a cikin al-Kur'ani, to wannan umarni ya zama tilas. Saboda haka, a yanzu da ake kera makamai iri-iri, to, wajibin Musulmi ne su zama su ma sun mallaki makamai iri-iri, wanda idan kafirai suka yi musu farmaki, za su yi maganin farmakin nan da wannan tanadi da suka yi na daga kerarrun makamai sababbi. Ko da nan gaba kuma za a kirkiro sababbin makaman da ba a san irinsu ba, to, wajibi ne Musulmi su mallaki irinsu domin su yi maganin farmakin da Arna za su yi musu.

Da Allah (S.W.T.) Ya ce: "Ku yi musu tanadin abin da kuka sami iko na daga karfi…" wannan yana nuna mana cewar wajibin Musulmi ne su yi tanadin karfi wacce za ta zama ta shiriritar da dukkanin dabaru na kafirai. Mu sami tanadin karfi wanda zai warware dukkanin mugunyar tanadi da arna suka yi. Saboda haka, a duk lokacin da aka daga tutar "La Ilaha, Illallah, Muhammadur Rasulul-Lah!" a duk lokacin da aka daga tutar Jihadi domin daukaka kalmar Ubangiji, domin kuma a bude hanyar Ubangiji a bayyana Addinin Allah, a yi aiki da Shari'ar Allah, kuma Musulmi wadanda za su yi wannan Jihadi suka tsarkake niyyarsu; imma dai dayan biyu ya abku a garesu, ko dai nasara, ko kuma shahada. To, idan Musulmi suka fita da wannan niyyah, Wallahi sai an taimakesu, sun ci nasara gagaruma akan abokan gabarsu, sannan a samu wadansu Allah Ya ba su arzikin shahada. To, wanne ne na ki a cikin wadannan guda biyun; Nasarar, ko kuma shahadar? Yana daga cikin babban burin kowane Musulmi na kowane zamani ya zama cewar ko dai ya sami nasara akan abokan gaba, ko kuma ya yi shahada a tafarkin Allah.

**Sirrin Makiya**

Ya 'Yanuwa Musulmi! Wajibi ne ku gane sirrin makiyanku na daga Yahudawa da 'Yan Mishan, da 'Yan Kwaminis. Wadannan mutane, babu wanda ya fi su tsoro. Idan fito-na-fito za mu yi da su; su kalli kirjinmu, mu kalli nasu, to, a duniya ba a taba samun mai jin tsoro ba sama da kariribа. Idan dai Musulmi suka yi kyakkyawar niyyah, to, sai Allah (S.W.T.) Ya taimakesu su kurmushe duk tawayen da kafiri zai yi. Duk kuma kaskancin da kafiri zai nuna wa Musulmi, to, idan dai Musulmi suka tsarkake niyyah, Allah (T.W.T) zai ba su rinjaye, da nasara, da galaba akan arna, har su samu su tsarkake kasar Ubangiji daga wasan kafirai, da kuma barnarsu. Har ya zamana al-Kur'ani ya zama shi yake da hukunci akan ban kasar Allah, kuma Sunnar Manzon Allah (S.A.W.) ta zama ita ke da fada a ji, kuma har ya zama na gaskiya da haske su bayyana a ban kasa; kuma duhu da karya duk su bata a ban kasa. Allah (T.W.T.) Ya tabbatar da haka a cikin al-Kur'ani, yana cewa " Wallahi sai Allah ya taimaki mai taimakonsa, kuma hakika Allah ma'abocin karfi ne da buwaya."

Taimakon Allah da wannan ayar ta yi magana a kai, shi ne mu taimaki Addininsa, domin ba mu da ikon da za mu iya taimakon Allah. Duk wanda ya taimaki addinin Allah, Wallahi sai Allah Ya taimake shi.

**Umarni Kan A Yaki Kafirai; Allah Zai Ba Da Nasara**

Saboda haka, ya bayin Allah! Ku yi Jihadi domin daukaka kalmar Allah, ku yaki wanda ya kafirce wa Ubangiji, ku yaki wanda ya hana a yi aiki da Shari'ar Musulunci. Saboda haka Allah (S.W.T.) Ya fada a cikin Surah al-Taubah, ayah ta 14-15, Ya ce, "Ku yakesu, Allah zai yi musu azaba da hannayenku, ya wulakantasu, Ya kuma ba ku nasara a kansu, kuma Ya warkar da zukatan mutane muminai; Allah kuma Ya tafiyar da bakin cikin Muminai, kuma Allah Zai yi gafara ga wanda ya ga dama. Allah masani ne kuma mai hikima." (Al-Taubah 9/14-15)

A wasu ayoyin, Allah (T.W.T.) Ya yi alkawari wa Muminai masu Jihadi cewa zai shiryar da su, kuma zai ba su nasara, Allah (S.W.T.) ya ce, "Wadanda suka yi Jihadi a tafarkinmu, tabbaci hakika sai Mun shiryar da su ga hanyoyinmu, kuma Allah Yana tare da masu kyautatawa."

**Sakamakon Kin Yin Jihadi; Kaskanci A Rayuwa**

Ya jama'a, ya bayin Allah! Ku san cewa barin Jihadi a lokacin da ya kama, zai sa Allah (S.W.T.) Ya damfara wa Musulmi kaskanci, saboda Musulmi ba su taba barin Jihadi ba a lokacin da ya kamata ba sai dai Allah Ya dora musu wannan kaskanci, ba zai cire shi ba har abada, sai lokacin da Musulmi suka dawo ga koyarwa ta Addinin Musulunci. Ma'aikin Allah (S.A.W.) ya ce, "Idan mutane suka yi rowar dinarinsu da dirhaminsu, suka yi ciniki da riba, suka zama sai kiwon shanu suke yi, sannan kuma suka bar Jihadi domin daukaka kalmar Allah, sai Allah Ya saukar musu da bala'i wanda ba Zai dauke musu shi ba har sai sun koma ga Addininsu."

To, Wallahi idan kun duba irin halin da muke ciki a yanzu, ba Musulmin Nijeriya kadai ba, a'a, Musulmin duk duniya, barin Jihadi shi ya kawo mana wannan kaskanci da muke ciki. Akwai kaskancin da ya shige fadan da Musulmi suke yi a junansu ya zamanto cewa arne ne zai yi musu sulhu? Fadan da ake yi a Afghanistan da Rasha, a Geneva aka yi sulhunsa; Fadan da ake yi a tsakanin Iran da Iraq, a Geneva shi ma aka yi sulhunsa; kuma Sarkin arna ne yake yin wannan sulhu.

Hakanan a yanzu, za ka tarar da idan Musulmi suna fada, 'yan sanda ne suke yin sulhu, wanda yawancinsu duk arna ne. To, yanzu akwai kaskancin da ya fi haka? Ga shi kuwa Allah (S.W.T.) Ya na cewa, "Idan Jama'ar Muminai guda biyu suka yi taho-mu-gama, to, ku (Musulmi), ku yi sulhu a tsakaninsu…" (Al-Hujurat 49/9).

To, amma da aka bar Jihadi, sai ya zamana arna ne suke yin wannan sulhu a tsakinin Musulmi, a maimakon su Musulmin su yi sulhu a tsakaninsu kamar yadda Allah (S.W.T.) Ya bayyana.

**Yadda Musulmi Ya Kamata Ya Kasance Ga Arna**

Allah (T.W.T.) Ya ce, "Ya ku Jama'ar da ta yi imani! Ku yaki kafiran da suke kusa da ku, kuma lalle ne su sami gallazawa daga gareku. Ku sani cewa Allah Yana tare da masu jin tsoronsa."

**MATSAYIN JIHADI GA MUSULUNCI**

Ya bayin Allah! Wajibi ne ku sani cewar Jihadi, shi ne tsororuwar Addinin Musulunci. Muddin babu shi, kamar Bijimin Sa ne wanda ba shi da tozon baya,

ballantana ma a samu tsororuwar tozon. Wato, bayansa ya zama kamar na jaki ke nan. To, haka Musulmi, a duk lokacin da ba su yin Jihadi, sun zama ke nan kamar jakuna sai dai a hau (Waliyadzu bil-Lahi). Saboda haka, Allah (S.W.T.) Ya yi umarnin da a yaki kafirai da munafukai. Ana yakin wadannan guda biyun ne ta hanyar matakai guda hudu:

**i.** **Yaki Da Zuciya** – Shi ne mu yi tunani akan cewa kafiran nan fa ba su gane Addinin Musulunci ba, kuma ba mu yi musu wa'azi ba.

**ii.** **Yaki Da Harshe –** Mataki na gaba bayan mun yi yaki da zuciya, shi ne sai mu fito mu yakesu da harshe, wato mu bayyana musu mene ne Musulunci da bambancinsa da kafircin da suke yi. Sannan kuma mu bayyana musu cewa mu ma fa muna iya rama gaba ga yakin da za a yi mana. Za mu yi haka ne duk da harshe.

**iii.** **Yaki Da Dukiya –** Duk abin da zai taimaki Jihadi na dukiya, da na baka, da na fito-na-fito, mu saye shi da kudinmu.

**iv.** **Yaki Na Fito-Na-Fito –** Wannan shi ne matakin Jihadi na karshe. Bai halatta ba ya zamana mu ne muka fara dukan arna, ko ya zamana cewa mu ne muka fara far musu ba. Amma duk wanda ya far mana, to, ba zai share ba. Ma'aikin Allah (S.A.W.) sai da ya yi shekara goma sha uku (13) yana wa'azi. Idan an mare shi a kuncin dama, sai ya bayar da na hagu. To, mu ma haka muke so mu yi da kafiran kasar nan, amma hakkinmu, kamar Shari'ah, babu wanda ya isa ya take mana, ko da jininmu zai cika kasar nan aikin gudana.

Saboda haka, idan a da ba mu gane Shari'ah ba, to, yanzu har a kauye an gane Shari'ah, cewar Shari'ah, ita ce numfashin Musulmi; idan babu ita, to, mun zama matattu. Saboda haka, wadannan matakai, wajibi ne Musulmi su yi aiki da su a kowane hali.

Saboda haka, za a yaki kafirai da dukiya, da makamai, za a yaki Munafukai da hujja, da cacar-baki – suna kawo dalilinsu, muna kawo namu. Idan mutum yana yaki da munafuki, to, kada ya bar shi ya yi ta surutu, ba tare da ya ba da amsa ga duk kalmar da munafukin zai fada ba.

**DALLIN YIN JIHADI**

Allah (S.W.T.) Ya shardanta yin Jihadi ne domin ya zamana an daukaka kalmarsa a ban kasa, ta yadda ba za a bauta wa kowa ba sai Shi (S.W.T.). Wajibi ne a cigaba da Jihadi har ya zamana a duniya Allah kadai ake bautawa; ba a shirka da Allah a komai. Allah (S.W.T.) Ya ce, "Ku yakesu, har sai an rasa fitina (kafirci da shirka). Kuma dukkanin addini ya zama ga Allah (S.W.T.) kawai."

Saboda haka, Allah (S.W.T.) Ya shar'anta cewa, wajibi ne a tsige kafirai da kafirci; kuma wajibi ne a tsige shirka da Mushrikai a ban kasa. Allah Ya bayyana dalilin yakin Musulmi da dalilin yakin kafirai. Allah (T.W.T.) Ya ce, "Jama'ar da suka yi imani, suna yin yaki ne domin daukaka kalmar Allah, amma wadanda suka kafirta, suna yin yaki ne domin daukaka kalmar gumaka. (Ku muminai), ku yaki abokan shaidan. Hakika makircin shaidan, raunanna ne."

Imam Ibn Al-Qayyim al-Jawziyyah ya ce, "Binciken da aka yi game da kalmar Jihadi, farilla ce akan kowane Musulmi; imma ya yi da zuciya, ko da harshe, ko da dukiya, sannan a yi yaki da hannu, da kuma karfi. To, wannan nau'i na Jihadi, ya wajaba akan Musulmi gwargwadon yadda zai iya."

Amma a yanzu abin ban haushi, za ka tarar da Musulmi da dama abokan sirrinsu ma arna ne, ba masa yin Jihadin zuciyar, wanda shi ne mataki na karshe, wanda idan mutum ya kasa yinsa, to, ba shi da Imani.

## HAKKIN DA ALLAH (S.W.T.) YA DORAWA KANSA

A wani Hadisin na Manzo Allah (S.A.W.), an ruwaito cewa Ma'aikin Allah (S.A.W.) ya ce, "Mutane uku, hakkin Allah ne ya taimakesu; (i) Wanda ya fita da niyyar yin Jihadi domin ya daukaka kalmar Allah; (ii) Bawan da ya ci alwashin ya fanshi kansa; (iii) Mai auren da ya yi niyyar yinh aure don kada ya yi zina."

Saboda haka, wadannan mutane guda uku, Allah (S.W.T.) ya wajabta wa kansa taimakonsu.

Saboda haka, ko dai mutum ya yi Jihadi, ko kuma ya ce, "Duk lokacin da za a yi Jihadi, to, sai na yi." To, idan mutum ya mutu da wannan niyyah, kuma bai yi ba, to, ba ya daga cikin wadancan munafukai. Saboda haka, ya jama'a mu saka wannan niyyah a ranmu.

Sannan wani Hadisin kuma ya ce, "Wanda ya mutu bai yi yaki ba, kuma bai zanta wa ransa cewa zai yi yaki ba, to, ya mutu, mutuwar maguzawa."

Sannan kuma Abu Dauda ya ruwaito cewa Manzon Allah (S.A.W.) ya ce, "Wanda ya mutu bai yi yaki ba, kuma bai sayi kayan tanadin yaki ya bai wa wanda zai yi yaki ba, sannan bai bar wanda zai yi yaki ba a cikin 'ya'yansa ko 'yanuwansa ba, to, sai Allah ya damfara masa wata muguwar musiba kafin Allah ya tashi alkiyamarsa." (Allah Ya kiyashemu, Amin!)